**Interview 8: Lawali Tankari, Mai Yankan Taya**

Mai Yankan Taya (MYT): Sunana dai Lawali Tankari. An…shekarata…ina da shekara talatin da bakwai. Sannan wannan aikin yankan taya ne. Muna yankawa muna sawa ga mototi haka. E. Akwai abubuwa da dama da muke yi. Ka gane, duka wad dai…ƙarhe wanda ya danganci mota inda take da sala…kaushu to zamu yank amu sa. Wurin da take da kaihi duka muna yankawa mu sa ciki. E. Duk suna unhwani da shi ha manya.

Int: Ha manya?
MYT: E. Ha manya suna unhwani da shi. Ƙanana tsakanin … waɗannan *couper de caler*, e…mi ake cewa da *dix neuf* duk suna aiki da shi. Su ko waɗancan su ..aa? *mille neuf cents vingt et quatre* (1924) ma duk kana aiki da su da motuna.
Int: Motuna ma suna aiki da su?
MYT: E. Motuna. Wurin baya wajen bulok na baya muna sa musu.

Int: E.
MYT: E. Yanzu wannan shi ne muna yanka shi mu sa shi da bara ta *dix neuf* (19). Ka gane? Ga bara ta *dix neuf* (19), in munka sa shi shi ke nan ya haɗu. Sai a darma ga mota.
Int: Mm.
MYT: Wurin bàrâ.

Int: E.
MYT: Bàrâ ma ba ta kusa ne da na gwada ma ita. A'a. Sai sun hiddo in suka hiddo muka gani sai mu ce wanga muna iya yin wannan aikin.
Int: Mm.
MYT: Ka gane?
Int: Mm.
MYT: In suka hiddo muka gani sai mu ce musu to wannan duk muna iya mu gyara musu shi. E. Insha Allahu.

Int: Mm.
MYT: Ko…haka nan na da yuƙaye muka kamawa muna yanka, muna ta koyo sai da munka tai muka iya. E. Lalle in ba dan da suka tai noma ba mun kai wajen mutum ashirin da suke koyo.
Int: Da suke koyo.
MYT: E. Sun tai noma na ko kama goma haka. Duk suna koyo na, sun tai noma na yanzu. Waɗannan ba swa yin makaranta. Su ba su makaranta. Da ba su makaranta na sai suna zowa nan aiki. A akwai wuya sai dai in mutum ya yi haƙuri sai ya iya. Akwai wuya. E. Akwai wani yana iya ma ya kai kusan shekara ma in dai ba shi yana tsayawa na ko da yaushe yana kai kusan shekara ma bai iya ba. Tun da ka ga ga wani nan dai shi shekara shi wajen huɗu ke nan. Yana nan ko aiki ma bai tahiya ko ina nan yake. E. Akwai yuƙa.

Int: Mhm.
MYT: Akwai adda (another male voice: Ni uwayena ba ni …).
Int: Mhm.
MYT: Ka gane?
Int: Ka ce akwai yuƙa amma in an ba ka yuƙa guda …
MYT: Ka ga ga yuƙa guda. Ba mu aska guda. Ka gane?

© Boston University

Int: Aska?
MYT: E. Aska. E. Da ita muke aiki muna huda. Magagari, *lime* guda. Ga *lime* ɗaya, na aiki dan da shi muke ɗaɗawa muna bugawa, haka. Aiki da shi.
Int: Kuna yankawa da shi?
MYT: E muna yankawa da shi. Ba ni marto babba. Wanga shi ne in ya kai wurin da ya kai da shi muke bugawa, muna hidda ha… E. Wannan seren bulok.

Int: E.
MYT: Da taya ne muke yankawa muna yin shi. Ban taya.
Int: Wace irin taya? Ta manyan motoci?
MYT: E. Ta katarpilar, wannan manya. Da ita muke yanka bai tun da ka ga ga taya can ma idan kana linƙanta.

Int: E.
MYT: Da ita muke yankawa muna yi.
Int: Mm.
MYT: Tayoyi sai mun yi bida tun da yanzu sun kai inda suka ƙare. A ana rasawa.
Int: Mm.
MYT: Ana samun lokacin da ake rasa su.
Int: E.
MYT: Sai an yi biɗa a samu. Daga nan Nijer dai muke neman su.

Int: Kuke nemansu.
MYT: E. Sabo da sai waɗanda aka kashe dan ka san na katarpilar tsada garesu ba mu iya sayensu haka.
Int: E.
MYT: E. To akwai mai ba mu wuya shi ne na relê, na babban mota. Shi wannan yana ba mu wuya ƙwarai. Wannan sai manya. E. Sai cikin yaran da suka yi kama shekara ukku suna aiki. Su ka iya yinsu amma ƙanana ba su iya wannan rele (some male voice: Salamu alaikum?).
A wannan aiki na maza ne kawai.

Int: Na maza ne.
MYT: Sabo da mata ba za su iya hanƙurin yinshi sabo da …mu in mun zamna nan sai ta hwaɗi muna iya zai… gudan ini nan.
Int: E.
MYT: In ana kawo muna ‘yan kuɗi ke nan ba mu iya tashi. Mace ko ka gani ba ta iyawa.
Int: Iyawa. Ihehehe!
MYT: Gaskiya. E. Ba …ba ni yuƙan nan ɗan baba. Mu ko wancan in gani. Ba ni wânnan. Mm. Wanga ya yi ƙarami. Ka ka ruwa kusa takwan.
Participant1: Shi na ni ce wai da ƙasa dai.
MYT: Yanzu zan hwara gwada ma yadda muke yi. Ka gane?
Participant2: Yanzu, yanka ne ake a daidaita?
MYT: Yanzu zan daidaita shi sabo da ku ga yadda muke yi. Daidaita shi zan yi yanzu shi komo. Wai muna yi muna aje waɗanga na. In suka zo suka tambaya sai mu ba su.
Int: E.
MYT: In sun zo, kowane da irin wanda yake so. Yanzu … E kowane da irin wanda yake so. Waɗannan rowansu ka sawa yuƙa ba ta kwasa zahi.

Int: E.
MYT: Ke nan sai ta yanka da kyau.
Int: Da kyau. Mm.
MYT: E. Ba ta kwasa zahi. Yanzu ka gan shi. Wanga shi muke sawa wurin baran *dix neuf*. E, muna ɗarmewa.
Int: Ana ɗarmewa?
MYT: E. Ana ɗarmawa. In ya shiga kawai sai a ɗaure. Ba mu wannan, ba ni shi ma in sa musu su gani. Ba ni marto. Ka gani?
Int: E.
MYT: Ka gani shi komi a yi gaban idon mutum, yarona ya yanka ya banshi.
Int: E.
MYT: Ni ko zan sawa sabo da na jima ina aikin.

Int: Mm.
MYT: Ga shi ka ganshi. Ka gani ya ƙare, in an je sa shi ɗai za a yi a …
Int: A ɗaure.
MYT: A ɗaure. Ka ga ga mai shi nan. Kai malami? Ga abinka.
Participant 3: An sallame ki.
Camera woman: Mhmmm.
MYT: Kawo wanga ana iya a yi jika biyu, haka. Akwai wanda ana yi jika…
Int: Ciniki ne kuna yi koko dai …
MYT: A’a ana magana ne. Kowane… ha na dala hamsin akwai.

Int: E.
MYT: Babu yadda ba a yi sabo da waɗanda ba su da ƙarhi ne ke zakkuwa. Ke nan wanda bai da ƙarhi kawai an san yadda ake mishi. E to ba a haɗa na Turawa da namu sabo da su da *machine* suke yi. Mu ko wanga muna abunga ne. Su nasu yana iya shekara biyat ko…mu ko namu ko ya yi yawa bakin shekara ɗaya. Amman waɗanga mutane waɗanda ke yi kwaikwayon Turawa irin na Najeriya waɗannan su ba su jimawa da an sa sabo da shi sunka hi son namu.

Int: E.
MYT: Da sun … da an sa nasu kawai bai kwana biyu ya cire.
Int: E.
MYT: Waɗannan Ibo-Ibo da a akwai cikin garin nan. Da an sa nasu kwana biyu ya cire ba su yi. Shi ya sa suke anhwani da namu, wannan nasu yana da wuya. In dai kaushu na ba su hana anhwani da shi. Lalle yana da … bai da musali.

Int: E.
MYT: Sabo da yana iya yin shekara ɗaya, wani bi kuma ba zai kai shekara ba. E. Amman muna gaya musu dai shina shekara dai sabo da in ruwa suna sabka, ke nan yana saurin…yana mutuwa haka. Amman dai muna ba su, muna gaya musu kan shekara ɗaya. Lalle suna bukatassu sosai sabo da kullum dai in munka hito muna samun abin da zamu ci da yaranmu. E. Insha Allahu. Muna biyan guntayen buƙatocinmu duka waɗanda in sun samu. Ha gobe ma, ha gobe suna buƙata. Shi ne ni ce maka. Ka ga ga wani nan dai ya kawo. E.